# HUKUNCE-HUKUNCE DA LADDUBOBI 10 A YAYIN KETARE HANYA

# (أحكامٌ وآدابٌ شَرْعيةٌ في المُرور)

**Tattarawar:** Dr. Haisam dan Muhammadu Jamil Sarhaan

Tsohon Malami a Ma'ahad wanda yake Masallacin Annabi mai daraja, kuma kulawa da makarantar Ma'ahadus Sunna

**Tarjamar:** Dr. Abubakar Hamza Misau

Yana daga ayoyin Allah Ta'alah masu girma: yadda ya shumfuda mana kasa ya saukake ta, domin mutane su iya rayuwa akanta da bulaguro, Allah Ta'alah ya ce: "**(ALLAH) SHINE WANDA YA SANYA MUKU KASA A SHUMFUDE, KUMA YA SANYA MUKU HANYOYI A CIKINTA, DOMIN KU SHIRYATU**" [Zukhruf: 10].

Kuma yana daga godiyar ni'ima: a kula da hukunce-hukuncen da shari'a ta zo da su, a yayin ketare ko shigewa ta kan hanyoyi, **Daga cikinsu**:

**1-** Kada da abin hawanka, ka ketare iyakar gudun da aka yi izini, ko ka tsallake danjar hanya, domin kada ka jefa rayuwarka ga halaka, da ta wadanda suke kewaye da kai.

**2-** Runtse idanu daga kallon mata akan hanya, da nisantar tabo su da magana ko jikinsu ko mutuncinsu, kuma ka tuno cewa, kai ma kana da uwa da 'yar'uwa da 'ya, wadanda kake kin wani ya takura musu.

**3-** Kada ka cutar da sauran mutane ta hanyar kure karar rikodar a daidaitarka ko mota, Annabi SAW yana cewa: "**WANDA YA CUTAR DA MUSULMAI A HANYARSU, TO TSINUWARSU TA TABBATA AKANSA**" (Hadisin Dabaraniy: 305, kuma Albaniy a cikin Sahihul Jami' yace hadisi ne hasan: 5923).

**4-** Kada ka wurga dukkan abinda zai cutar da masu tafiya akan hanya, na dauda ne ko wanin haka, Sahabiy Abu-Barzata (R.A) ya ce: "**YA ANNABIN ALLAH, KA SANAR DA NI WANI ABU DA ZAN AMFANA DA SHI? SAI YA CE: KA KAUTAR DA ABU MAI CUTARWA DAGA HANYAR MUSULMAI**" (Muslim: ).

**5-** Don haka, idan akan hanya ka ga abinda zai cutar da matafiya, kamar dutse ko kashi to ka kau da shi gefe guda, saboda aikata hakan aiki ne mai kyau, Annabi SAW ya ce: "**WANI MUTUM YA SHIGE RESHEN WATA BISHIYA AKAN HANYA, SAI YA CE: WALLAHI ZAN KAWAR DA WANNAN DAGA HANYAR MUSULMAI, TSORON KADA YA CUTAR DA SU, SAI AKA SHIGAR DA SHI ALJANNAH**" [Muslim: 1914].

**6-** Ka bi a hankali a yayin cunkoso da wurin danjar dakatar da motoci; kada ka hana na bayanka tafiya, kuma kada ka furnace wanda yake gabanka, Annabi SAW ya ce a lokacin da ya ji yadda ake fafarar rakuma, a yayin barin farfajiyar Muzdalifah: **YA KU MUTANE! INA**

**HORARKU DA KU TAFI CIKIN NATSUWA, SABODA BIYAYYA GA ALLAH BA SHINE ZABURARWA DA SAURI BA”** (Bukhariy: 1670).

**7-** Don haka, ma’abucin mota yana da hakki akanka, sai ka zama mai kula da shi, domin kasancewarsa makobci ne mai lokaci, kuma lallai makwabci yana da hakkinsa, sawa’un makwabci ne zaunanne, ko wanda yake da kayyadaden lokaci mai shigewa.

**8-** Kuma duk wanda shine yake da hakkin cancantar fara wucewa a shata-le-tale, ko a jikin danjar hana ketarewa, to ka buda masa, domin hanyoyi hakki ne na kowa, shi kuma wannan yana da damar fara wucewa saboda rigaye.

**9-** Ka bi tare da aiki da dukkan tsare-tsaren da suke kawo salama, da kiyaye haddura, kamar daura belt din mota, da seta madubin hango abinda yake baya.

**10-** Kuma ka lura da kuskuren tukin da waninka zai yi, saboda hakan ka iya cutar da kai.

**11-** Don haka, ka yi riko da tsare-tsare da dokokin kan hanya, domin kiyaye lafiyarka da lafiyar wadanda suke kewaye da kai, kana mai biyayya ga shugabanninka, kuma ka yi tawakkali ga Allah, a cikin zamanka da bulaguronka, da hawanka ga abin hawanka da saukanka, domin Allah ya kewayeka da kiyayewarSa da kulanSa, Allah Ta’alah ya ce: “**KUMA KA YI TAWAKKALI GA ALLAH, KUMA ALLAH YA ISAR MAKU; WAKILI**” [Ahzab: 3].

**Tarjamar Dr. Abubakar Hamza Misau, Ramadan 1444 = 2023**